


An yi wasu yara biyu.

Sunansu Sale da Bukar.

Sale da Bukar na da


ƙwaɗayi.



Maman Sale ta yi masa gargaɗi.

Sale bai ji gargaɗi ba.





Maman Bukar ta yi masa gargaɗi.


Bukar bai ji gargaɗi ba.



Wata rana wata aljana ta shiga gari.

Aijana ta zo a sifar tsohowa.


Tana shigowa ta yi satar yara.



Aljana na da kwando.

Kwando na cike da kayan marmari.

Yaran gari sun guje aljana.




Sale da Bukar sun je gun aljana.

Ga kayan marmari

daban-daban a kwando.

Sun ɗauka sun kai baki.



Kwastam sai wata guguwa ta tashi.

Kwandon aljana ya kife.

Kayan marmarin ciki sun zama kunama.



Sale da Bukar sun gudu gida.

Sun koyi darasi.